SANAD

# RUBUTU GAME DA CANZA FAHIMTA DA QAGE



LITTAFI NA DAYA

1

CANZA MA'ANA FADIN ALLAH MADAUKAKIN SARKI :
( DUK WADANDA BASUYI HUKUNCI DA ABINDA ALLAH YA SAUKAR BA WADANNAN SUNE KAFIRAI )
SURATU MA'IDAH 44
A WURIN KUNGIYOYI MASU GURBATACCIYAR FAHIMTA.

H Takaitaccen Bayani na (1) Gaba ta (105) Bugu na biyu 2019

Da sunan Allah mai rahma mai jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikai, tsira da aminci sun tabbata akan mafificin annabawa da manzanni shugabanmu annabi Muhammad tare da iyalansa da aminansa baki daya.

## Nazari game da gurbatacciyar fahimta

Mene ne ma'anar fadan Allah madaukakin sarki ?

( duk wadanda basuyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba wadannan sune kafirai) 44(azzalumai) ( fasikai)47 [1]

Shin kana tunanin maanar wannan ayar shine kwadaitarwa akan tabbatar da hukuncin Allah koda ta hanyar yaki ne ? shin kana tunanin afkuwar yaki tsakanin musulmai domin tabbatar da wannan aya ? saidai kash!! Wasu sun fahimci hakan !, su waye suka fahimci wannan aya ta wannan fuskar ? ta ya suka fassarata ? shin ingantacciyar fahimtace?

Malaman kungiyoyin masu gurbatacciyar fahimta da sunan musulunci suna ganin duk wanda baya hukunci da shariar ubangiji kafiri ne da ya wajaba ayakeshi kuma ya halasta a kasheshi, haka duk wanda ya zabi wani wanda baya hukunci da shariar Allah kafiri ne.

Wanda ya sanya kundin tsarin mulki(constutions) shi yake hukunci acikin al'amarinsa mushiriki ne ga Allah madaukakin sarki ! tushen wannan hukunci shine fahimtarsu da sukayiwa ayar{ duk wadanda basa hukunci da abinda Allah ya saukar wadannan sune kafirai }




### Me gurbatacciyar fahimtar ta haifar ?

- Kafirta mafi yawancin musulmai da suffantasu da jahilai mushrikai
- Kira ga kafirta shuwagabannin musulunci.
- Bayyanar kungiyoyin kafirta musulmi da kira zuwa jihadi da fadaduwarta har zuwa ga Da'ish a wannan zamani.
- Halasta kashe-kashe da zubar da jini da sunan hukunci da abinda Allah ya saukar.

١ – المائدة آية (٤٤، ٤٥، ٤٧)



## ABU AALA AL-MAUDUDI 1321 -1399 AH 1903- 1979 AC

Gaban farko.

Inda ya fadi fahimtarsa game da ayoyi guda uku da suke dauke da hukuncin Allah mai girma da buwaya yace : tabbas Alkur'ani yana cewa lallai duk wani hukunci sabanin hukuncin ubangiji baza'a kirashi da kuskure ko haramun ba kadai, sai dai ma a kirashi da kafirci da bata da zalunci gami da fasikanci kai duk wani hukunci irin wannan, hunkunci ne na jahilci, imanin mutum bazai taba cika ba indai bai kafirce mashi ba .[2]



## Sayyid Kudub 1324 -1386 AH 1906- 1966 AC

Gaba ta biyu

Yana daga manyan ra'ayoyin Sayyid Kudub fikiratul hakimiyya (kafirta duk wani hukunci da ba na Allah ba) da ya samota daga fahimtar Abu Aala Al-maududi. Saidai shi ya kara fadadata inda ya gina abubuwa masu matukar hadari. Ya sanya ra'ayoyinsa masu hadari wajen fassara ayoyin, ya maidata kadhiya ta akida a musulunci ya kafirta duk wanda bai hukunci da abinda Allah ya saukar ba, koda ya gaskata hukuncin Allah gaskiya ne, kuma wahayi ne daga Allah.[3]
Kamar yadda hakan ya fito fili wajen fassaran sa a fadi Allah madaukakin sarki { duk wadanda basuyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba wadannan sune azzalumai}
Inda yake cewa : wannan suffar(azzalumai) batana nufin wani hali ne wanda ya sabama suffar data gabata ta kafirci ba a fadin Allah madaukakin sarki { duk wadanda basuyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba wadannan sune kafirai} saidai Karin bayani akan wanda bai hukunci da abinda Allah ya saukar ba, kafiri ne sabida yayi watsi da kadaituwar ubangiji da bauta da kebantuwarsa wajen sanya ma bayinsa doka da yin watsinsa da fadin Allah shine ya cancanta a bautamasa kuma shine ya cancanci sanyawa mutane doka.[4]



## Muhammad kudub 1435 -1337 AH 1919- 2014 AC

gaba ta uku:
karfafawa da goyan baya.

Hukunci bada abinda Allah ya saukar ba da yarda da shari'ar data sabama abinda Allah ya saukar dukansu suna warware imanin mutum (la ilaha illa Allah ) sabida hakama aya ta sauka wajen yanke hukunci akan haka cewa { duk wadanda basuyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba wadannan sune kafirai} [5] suratul ma'ida
Duba irin wannan gurbatacciyar fahimta wacca ta sabama fahimtar magabata game da wadannan ayoyi ta wannan fuska mai ban mamaki, akarshen zamani, wacca ta jawo akaitama al'ummar musulmi da shuwagabaninsu hukunci da jahilci da kafirci !

٢ - الخلافة والملك أبو الأعلى المودودي |
٣- انظر ظلال القرآن لسيد قطب٢|٨٨٧ ١٧
٤ - ظلال القرآن ١٢ ٩٠٠
٥- - مفاهيم يجب أن تصحح |١١٨

## Daidaitacciyar fahimta

Shin fahimtar data gabata tayi dadai da koyar annabi da fahimtar sahabbai da magabata na kwarai da fahimtar malamai ?

YADDA FAHIMTAR AYAR TAKE A ZAMANIN ANNABI



**A ina ayar ta sauka akan wane ta sauka ?**

Ayar data gabata ta sauka a Madina ne lokacin da yahudawa suka tambayi manzo tsira da amincin Allah su tabbata gareshi akan hukuncin mazinata ma'aurata , dukanin ayoyin sun saukane akan kafirai [6].

Fassarar masanin Alkur'ani kuma malamin al'umma : Sayyuduna Abdullahi dan Abbas 17 H

Dawus ya ruwaito daga wurin dan Abbas fadin Allah cewa { duk wadanda basuyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba wadannan sune kafirai} suratul ma'ida Yace " ba kafirci da suka fahimta bane" awani fadin kuma " kafirci ne wanda baya sarayar da musulunci" awani fadin "butulci ne dabekai kafirci ba, zalunci ne dabekai kafirci ba, fasikanci ne dabekai kafirci ba"[7]

### Bincike akan ingancin ruwayar ko rashin ingancinta.

- Kalu bale na farko : sanadin ruwayar data gabata akwai Hisham dan Hujairi aciki, wasu malamai sun raunatashi ?
- MAIDA MARTANI : Ya isa hujja cewa Imamu Bukhari da Muslim suna kafa hujja da Hisham dan Hujairi acikin ingantattun littafansu, sannan kuma Imamu Sufyan al-sauri ya ruwaito irin ruwayar Hisham dan Hujairi, sannan Imamu Sufyan dan Uyaina yayi ruwaya daga gareshi[8].
- Kalu bale na biyu : " fadin cewa butulci ne dabekai kafurci ba" maganar Dawus ce ba maganar dan Abbas ba kamar yadda ruwayar Abdulrazzak ke nunawa?
- Maida martini : wanda ya ruwaito wannan Magana daga dan Abbas shine Sufyan dan Uyaina, kuma yafi Abdulrazak kyautata ruwaya sabida haka ake gabatar dashi, kuma wannan itace ruwayar Hakim acikin mustadarak wacca ya ingantata,sannan Imamu al-zahabi yayi mashi muwafaka akan hakan[9] .

SHIN AKWAI WADANDA SUKA KALU BALANCI FASSARAR IBN ABBAS GAME DA AYAR KUMA MAYE MA AUNINSA?



**Wannan kalu balen mai raunine baza'a kafa hujja dashi wajen mayarda fassarar dan Abbas ga wannan ayar ba .**

SAKAMAKO

٦- أسباب النزول ١|١٩٥، لأبي الحسن علي الواحدي النيسابوري ٤٦٨ه . زاد المسير ١|٥٥١ . لأبي الفرج عبدالرحمن الجوزي ٥٩٧ه . مسلم٣|باب رجم اليهود أهل الذمة |١٧٠٠ .
٧- أخرجه محمد بن نصر المروزي٢٩٤ه في كتاب (تعظيم قدر الصلاة ) ٢|٥٢١|٥٧٤|٥٧٥ .
٨- تهذيب التهذيب - (٣٤ / ٣٣)
٩- أخرجه الحاكم في المستدرك (تفسير سورة المائدة ) ٢|٣٤٢١٣|حديث :٣٢١٩

## Ya manyan malamai suka fahimci wannan aya ?

**Imam Ahmad bn Hanbal** 341 h.

Isma'il dan Sa'ad yace : na tambayi Ahmad game da fadin Allah madukakin sarki cewa { duk wadanda basuyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba wadannan sune kafirai} nace : wannan wana irin kafirci ake nufi ? yace " kafirci ne wanda baya fitar da mutum a addini "[10]

**Imamu Ibn Abdulbar** 463 h.

" Malamai sunyi ijma'i akan cewa zalunci acikin hukunci babban zunubi ne ga duk wanda yayi hakan yana sane da gangan, an ruwaito maganganu masu tsanani daga magabata akan hakan. Allah mai girma da buwaya yace : ( duk wadanda basuyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba wadannan sune kafirai) (azzalumai) ( fasikai) ayan ta sauka akan Ahlul kitabi ne (yahudu da nasara) Huzaifa da Ibn Abbas sunce : ta hada harda mu : sukace ba kafirce bane da yake fitar da mutum daga musulunci in wani daga cikin wannan al-umma ya aikatashi sai idan ya kafirce wa Allah da Mala'ikunsa da Littafansa da manzanninsa da kuma rana ta karshe "[11]

**Imamu al-kurdubi** 671 h.

" fadin Allah madaukakin sarki ( duk wadanda basuyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba wadannan sune kafirai) khawarijawa suna kafa hujja da zahirin wannan ayar suna kafirta mai aikata zunubi, wannan ba hujja bace , sabida ayar ta sauka ne akan yahudawa masu canja maganar Allah madaukakin sarki, kamar yadda hadisi yazo akan hakan , sune kafirai , wanda sukai tarayya a hukunci da wanda ayar ta sauka akansu[12].

### Shin ko mafi yawancin malamai sunyi muwafaka da fassarar da Ibn Abbas yayima ayar ?

Fahimtar mafi yawancin malaman musulunci ga ayar tayi daidai da fahimtar sayyuduna Abdullahi Ibn Abbas cewa ( butulci ne wanda bekai kafirci ba) wanda yayi hakan bazai kafirta ba, daga cikinsu akwai : ga wasu daga cikinsu

Abdulrazak Ibn Himam alsan'ani acikin tafsirinsa 211

Al-mam Abu muzfar assam'ani

١٠ - سؤالات ابن هانئ ٢/١٩٢ .
١١ - التمهيد ٥/٧٤ .
١٢ - المفهم لما أشكل من تلخيص مسلم، لأبي العباس أحمد القرطبي ٢/١١٦ .

## GURBATACCIYAR FAHIMTA

| | |
|---|---|
| Muhammad Ibn Nasru Al-marwazi | acikin Ta'azimu qadrussalati 516 |
| Abdulhak Ibn Adiyat Al-andalusi | acikin almuharar alwajiz 541 |
| Abubakar Muhammad Ibn Abdullah Al-muafiri | acikin Ahkamu Alqur'an 543 |
| Abu Al-faraj Ibn Aljauzi | acikin Zadul masir 597 |
| Muhammad Ibn Umar altaimi Albakari Alrazi | acikin tafsirinsa 606 |
| Alhassan Ibn Mas'ud Albagwi | acikin Mu'alamu altanzil 516 |
| Abdullah Ibn Ahmad Alnasfi | acikin tafsirinsa 710 |
| Ahmad Ibn Taimiyya | acikin fatawa738 |
| Aliyu Ibn Muhammad | acikin Tafsiru alkhazin 741 |
| Muhammad Ibn Yusuf Ibn Hayyan Al-andalusi Aljaini Alnafri | acikin tafsirinsa Albahrul almuhid 745 |
| Muhammad Ibn Muhammad jizzi alkalbi algamadi | acikin Altashil fi ulumi altanzil 757 |
| Abu Ishaq Ibrahim Ibn Musa Alshadibi | acikin littafinsa Almuwafaqat 790 |
| Ibn Abi al-iz Alhanafi Aliyu Ibn Ala'i aldin aldimashqi | acikin sharhi Akidatu aldahawi 793 |
| Alqadhi Abu alsa'ud | acikin tafsirinsa 983 |
| Muhammad Aliyu Alshaukani | acikin fathulkadir 1355 |
| Muhammad Sadiq Khan | acikin Fathhulbayan 1307 |
| Ahmad Mustapha Almuragi | acikin tafsirinsa 1371 |
| Alsheikh Abdulrahman Ibn Nasir Alsa'adi | acikin tafsirinsa 1376 |
| Muhammad Al-amin Alshanqidi | acikin tafsirinsa Adhawa'u albayan 1393 |

Bayan wannan maganganu na wasu malamai daga cikin Ahlul sunnah waljama'a , fahimtar malaman wannan zamanin ta sabawa fahimtar masu kafirta wanda be hukunci da abinda Allah ya saukar ba , kamar Sheikh Albani acikin littafinsa ( silsilatu sahihu Albani 6/106 da Ibn Usaimin acikin Altahzir min fitinati altakfir 68)

# *A Takaice*

## SAKAMAKON GURBATACCIYAR FAHIMTA

- Ta sabbaba masu ketare iyakokin sharia har suke kafirta shuwagabannin musulmai.
- Suna kafirta duk wanda ya yarda da hukuncin wadannan shuwagabannin da kai kara garesu ko yayi shiru akan hakan
- sun sabama fahimtar magabata na kwarai daga cikin sahabbai da tabi'ai da kuma malaman musulmi.
- Ya jawo yaduwar yake-yake da halasta zubar da jini da kasha rayuka da kuma fadan cikin gida da sunan raya khalifanci da hukunci da abinda Allah ya saukar.

## SAKAMAKON FAHIMTAR MALAMAN AL-UMMAR MUSULMI .

- Wannan gurbatacciyar fahimta tayi daidai da fahimtan khawarijawa na karnin farko.
- Wanda yake hukunci bada abinda Allah yasaukar ba da gangan yana aikata babban zunubi ne da Allah zai hukuntashi akansa.
- Mai aikata hakan bazai fita daga musulunci ba.
- Wanda yake aikata hakan musulmi ne kasheshi haramun ne.
- Ya zama wajibi akan malamai suyi mashi nasiha da nuna mashi hanya madaidaiciya .

**" Kasani cewa khawarijawa suna kafa hujja da wannan aya, cewa duk wanda beyi hukunci da abinda Allah ya saukar ba kafiri ne, amma malaman Ahlussunna sunce bazai kafirta ba dan beyi hukunci da ayar ba"[13]**

Imam Sam'ani acikin tafsirinsa 13 – 42/2

١٣ - تفسير الإمام السمعاني ٢/٤٢

# RUBUTU GAME DA CANZA KYAKKYAWAR FAHIMTA DA QAGE

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi yace:(akoda yaushe akwai malamai adilai da suke dakon wannan ilmin, suna kore masa canjawar masu wuce gona da iri, da kuma kagen mabannata da tawilin marasa ilmi.)[1]

Wasu masu gurbataccen tunani sun fahimci maganar Allah madaukakin sarki ta mahanga wacca batayi daidai da hanya ta ilmi da aka gada daga magabata na kwarai ba, kuma be daidai da manufofi da dabi'u masu girma na maganar Ubangiji ba

Suka fassara wasu ayoyi na Alqur'ani mai girma da suka sauka akan wanda ba musulmai suka ajeta akan musulmi

Suka dauki ayoyin da suke magana akan wasu kebantattun mutane, suka maida hukunce hukuncenta akan gama gari, suka canja ma'anonin zancen Allah ta wata fuska wacca ta gadar da mummunar fahimta a kwakwalen al 'ummar musulmi, wanda hakan ta haifar da gurbatattun dabiu da ayyukan da basu da alaka da addinin musulunci

acikin wannan shiri zamu fahimci canji da masu wannan gurbataccen tunani sukayiwa ayoyin Alkur'ani mai girma, da nisantarsa ga fahimtar annabi tsira da amincin Allah sun tabbata gareshi, da magabata na kwarai da kuma shariar musulunci

١-حديث مشهور صححه ابن عبد البر ، وروي عن أحمد بن حنبل ؛ أنه قال : هو حديث صحيح .


دار الفقيه
DAR AL FAQIH

مؤسسة طابة
Tabah Foundation
www.tabahfoundation.org

مبادرة سند هي إحدى مبادرات مؤسسة طابة للأبحاث والاستشارات

www.sanad.network
facebook.com/sanadnetwork
twitter: @sanadnetwork
youtube.com/sanadnetwork
instagram.com/sanadnetwork